Dandalin Sadarwar Zamani da Rabawa

Mahalarta taron za su yi tunani game da sirrin dangane da yanda suke raba bayani da kuma yin magana da wasu ta intanet, musamman dangane da yin amfani da dandalin sadarwar zamani. Za su iya yin bayani game da abun da aka musanya a cikin sirri a abubuwan dandalin sadarwar zamani sannan ka ƙara sani game da yanda ake yin amfani da saitunan sirri a intanet daidai.

Amfani da Dandalin Sadarwar Zamani

Kashi na Ɗaya

Tattaunawa a Aji

Kafin wannan aikin, ƙwaƙwasa alamar “YARDA” da “RASHIN YARDA” a gefen da ke kishiya da juna na ɗakin. Ba mahalarta taron damar sanin cewa da zarar ka karanta kowane bayani, ya kamata su kasance a gefe ɗaya ko kuma ɗaya gefen gwargwadon yanda suke jin ƙarfi; haka kuma mahalarta taron za su iya tsayawa a tsakiyar alamu guda biyu idan ba su tabbatar ba / ba su yanke shawara ba.

A tsakanin bayanai, nemi mahalarta taron su yi bayani game da matsayinsu sannan ka sanya ƙungiyar cikin gajeruwar tattaunawa game da kowane batu.

Sanar da Ɗalibanka

Zan karanta bayanin. Idan ka amince ɗari bisa ɗari, koma ga alamar “YARDA”. Idan ba ka amince gaba ɗaya ba, koma ga alamar “RASHIN YARDA”. Idan ba ka da masaniya ko kuma ba ka yarda ba / ki amincewa ga ɗaya, tafi tsakiyar matsayin da ya wakilci matsayinka da kyau.

Ina da asusu a dandalin sadarwar zamani kamar Facebook, Twitter, Snapchat ko Instagram.

Ina yin amfani da dandalin sadarwar zamani kowace rana.

Furofayil ɗina na dandalin sadarwar zamani — a kan dandalin sadarwar zamanin da na fi amfani da shi — na kowa da kowa ne.

Ina da abokai daban-daban / mabiya / abokan hulɗa (a wasu kalmomin, masu sauraro mabambanta) a kan dandalin sadarwar zamani daban-daban da nake yin amfani da su.

Mutanen zamanina suna da hanyoyi daban-daban da suke yin tunani game da bayanan da aka raba a dandalin sadarwar zamani idan aka kwatanta da manya.

Ina yin amfani da dandalin sadarwar zamani daban-dan wajen aikewa da wasu nau’in bayani.

Matakin Buƙatar Ƙara Aboki

Kashi na Ɗaya

Sanar da Ɗalibanka

Dandalin sadarwar zamani wani dandali ne a kan intanet da za ka iya yin amfani da shi domin ka haɗu da mutane da kuma yin hulɗa da su.

Tambayi Ɗalibanka

Wasu dandalin sadarwar zamani ne ka ji labari a kan su?

Kashi Na Biyu

Tattaunawa a Aji

Kafin waɗannan ayyukan, ƙwanƙwasa alamar “YARDA” da “RASHIN YARDA” a gefen da ke kishiya da juna na ɗakin. Ba mahalarta taron damar sanin cewa da zarar ka karanta kowane bayani, ya kamata su kasance a gefe ɗaya ko kuma ɗaya gefen gwargwadon yanda suke jin ƙarfi; haka kuma mahalarta taron za su iya tsayawa a tsakiyar alamu guda biyu idan ba su tabbatar ba / ba su yanke shawara ba.

A tsakanin bayanan, kasance a cikin gajerar tattaunawa a ƙungiyar ta hanyar yin amfani da tambayoyin da ke ƙasan kowane bayani.

Sanar da Ɗalibanka

Zan karanta bayanin. Idan ka amince ɗari bisa ɗari, koma ga alamar “YARDA”. Idan ba ka amince gaba ɗaya ba, koma ga alamar “RASHIN YARDA”. Idan ba ka da masaniya ko kuma ba ka yarda ba / ki amincewa ga ɗaya, tafi tsakiyar matsayin da ya wakilci matsayinka da kyau.

Don wannan aikin, yi tunani game da asusun dandalin sadarwar zamani da ka fi amfani da shi sosai.

Tambayi Ɗalibanka

An saita furofayil ɗin dandalin sadarwar zamanina zuwa na kowa da kowa.

1. Shin wannan ya canza hanyar da kake yin aike a kan intanet? Ta yaya? Ko kuma in ba haka ba, me zai hana?

Furofayil ɗina na dandalin sadarwar zamani na abokaina ne / mutanen da na sani sosai kawai.

1. Me yasa ka yanke wannan hukuncin?

2. Shin za ka aike da abubuwan daban-daban idan kowa da kowa zai gani? Wasu irin abubuwa?

Ina da aboki / mai bi / aboki a dandalin sadarwar zamani wanda ban taɓa haɗuwa da shi ba a zahiri.

1. Me yasa ka yi abota / ka bi / ka haɗu da wannan mutumin? Shin wani ne wanda ka haɗu da shi ta intanet, ko kuma ba ka taɓa ba?

2. Yaya za ka fayyace dangantakar?

3. Saboda ka yi hulɗa ta intanet kawai, shin ya yi tasiri a kan yanda ka yi hulɗa? Wasu alfanu ne a ka samu a kan irin wannan hulɗar? Wasu ƙalubale ne za a iya fuskanta?

Tambayi Ɗalibanka

Na amince da abokai duka / mai bi / buƙatar ƙara abokin da na samu.

1. Mene ne alfanun wannan hanyar? Wasu ƙalubale ne za a iya fuskanta?

2. Shin aboki / mai bi / buƙatar ƙara aboki na da muhimmanci idan aka yi mgana a kan sirrinka? Idan haka ne, yaya? In ba haka ba, me zai hana?

A duk lokacin da na haɗu da sababbin mutane, ina aika masu da buƙatar ƙara aboki / mai bi / buƙatar aboki.

1. Me yasa wannan ra'ayin yake da kyau / rashin kyau?

Na goge abokai / mabiya / abokan da aka haɗu da su.

1. Me yasa ka yanke wannan hukuncin?

Tambayi Ɗalibanka

A intanet, ina abota da / mabiyan / an haɗa ni da iyayena / masu kula ko malamai.

1. Shin wannan ya canza hanyar da kake yin aike?

2. Shin manya a rayuwarka sun taɓa yin jawabai a kan abun da ka aike da shi a

kan layi?

3. Wace irin moriya ce za a samu da / ko ƙalubalen zama abokai / mabiyan / haɗuwa da iyaye / masu bayar da kulawa ko malamai?

Abokan abokai / mutanen da ban haɗu da su kai tsaye ba a dandalin sadarwar zamai za su iya ganin wasu daga cikin abubuwa a kan furofayil ɗina.

1. Wasu abubuwa?

Na duba kuma / ko canza saitunan sirrinmu.

1. Mene ne ko kuma me zai hana?

2. Shin waɗannan saitunan sirrin sun yi sauƙi ko rikitarwa? Me zai sanya waɗannan saitunan sirri su yi sauƙin dubawa / canzawa?

Yaya Girman Hanyar Sadarwarka?

Kashi na Ɗaya

Sanar da Ɗalibanka

Yanzu, bari mu yi magana game da yawan masu sauraronka a dandalin sadarwar zamani.

Akwai manyan hanyoyi guda biyu dangane da yanda ake raba abubuwa (misali., hoto, bidiyo, aike mai ɗauke da rubutu) da mai sauraro. Na ɗaya, za a iya raba abubuwa tare da masu sauraro na asali, waɗanda za su iya zama abokanka / mabiya / waɗanda aka haɗa ka da su, ko kuma za su iya haɗawa da abokan abokai. Ni biyu, masu sauraronka na farko za su iya raba abubuwan tare da abokansu / mabiya / waɗanda aka haɗa su da su.

Za ka iya zaɓar masu sauraron da za su kusance ka amma akwai wahala sosai wajen kula da waɗanda masu sauraronka za su sake raba abubuwan da su / sake aikewa / sake yin tweeter.

Tambayi Ɗalibanka

Misali idan ka raba abubuwa da abokanka / mabiya / waɗanda aka haɗa ka da su, amma waɗannan bayanan ne dai suke raba su da abokansu / mabiya / waɗanda aka haɗa su da su, mutane nawa ne kake ganin kana rabawa da su?

Kashi Na Biyu

Tattaunawa a Aji

Rubuta waɗannan lissafin / sakamako a kan allo.

Sanar da Ɗalibanka

Bari mu yi wani ɗan lissafi. Idan, misali, kana da abokai guda biyu / mabiya / waɗanda ka haɗu da su a dandalin sadarwar zamani, kuma kowanne daga cikinsu yana da abokai guda uku / mabiya / waɗanda aka haɗu da su, mutane nawa ne, a matsayin mafi yawa (wasu abokan / mabiya / waɗanda aka haɗu da su ne suka zarta) za su iya ganin abubuwan da ka raba a dandalin?

1. Amsa: 2 a tare da 2 sau 3 = 8

Idan kana da abokai guda goma / mabiya / waɗanda ka haɗu da su a dandalin sadarwar zamani, kuma kowanne daga cikinsu yana da abokai guda goma / mabiya / waɗanda aka haɗu da su, mutane nawa ne, a matsayin mafi yawa, za su iya ganin

abubuwan da ka raba a dandalin?

1. Amsa: 10 a tara da 10 sau 10 = 110

Idan kana da abokai guda ɗari uku / mabiya / waɗanda ka haɗu da su, kuma kowannen su yana da abokai ɗari uku / mabiya / waɗanda aka haɗu da su, mutane nawa ne, a matsayin mafi yawa, za su iya ganin abubuwan da ka raba a dandalin?

1. Amsa: 300 + 300 sau 300 = 90,300

Sanar da Ɗalibanka

Waɗannan lissafin an yi su ne biga ga la'akari da cewa masu sauraronka na kusa da kai sun raba abubuwa tare da masu sauraronsu na kusa da su, amma babu wani ƙarin abun da aka raba bayan wannan. Duk da ha, a wasu lokutan, za a iya raba bayanai sosai baya ga waɗannan makusantar masu sauraron guda biyu.

Kashi Na 3

Tambayi Ɗalibanka

Yaya kake ji game da yiwuwar cewa mutane da yawa waɗanda ta yiwu ba ka sani ba (za ka iya sanin wasu daga cikin abokan abokanka) za su iya sanin abun da kake yi a kan layi cikin sauƙi? Mene ne zai iya zama naƙasu / ko mai yiwuwa na wannan ɓangaren?

Me yasa ka damu da wannan

Shin wannan ya canza yanda kake yin tunani game da raba abubuwa a kan layi? Mene ne ko kuma me zai hana?

Rabawa A Kan Intanet

Tattaunawa Ta Ɗaya

Sanar da Ɗalibanka

Za ka iya raba abubuwa a intanet tare da wani mai sauraron da ka nufa, amma a lokacin da ka sanya wani abu ya zama na kowa da kowa, zai iya jawo hankulan mutanen da ba a yi tsammani ba.

Abubuwan da aka watsa a kan intanet za su iya zuwa ”viral,” su watsu cikin sauri a sandalin dadarwar zamani, kasancewar sun yaɗu da kuma yiwuwar sun cakuɗu.

Tambayi Ɗalibanka

Shin wani zai iya yin tunani a kan misalin viral media?

1. In ba haka ba, nemi su yi tunani game da memes, remix, ko fitattun bidiyoyin da suka gani sannan / ko suka raba tare da abokai.

Yin hulɗa

Tattaunawa a Aji

Nuna wani misali na kwanan nan wanda aka danganta shi da / mahalarta taronka na cikin gida / wani abu a yankin don ci gaba da ƙarfafa manufa.

Tattaunawa Ta Biyu

Sanar da Ɗalibanka

Viral media zai iya yin kyau idan kana so ka jawo hankulan mutane zuwa aikinka. Duk da haka, jawo hankalin da ba a so zai iya haɗawa da cin mutunci da kuma ƙwarzaba ta intanet. Bidiyon sirri da ya fita ko aka raba ba tare da izini ba zai iya ɓata maka suna.

Tambayi Ɗalibanka

Ta wasu hanyoyi ne za a iya raba waɗancan abubuwa game da kai a kan intanet baya ga mai sauraronka da aka nufa, kuma ta yaya wannan zai yi tasiri a kanka / ko ɓata sunanka?

Zaɓuɓɓukan sirri na Dandalin Sadarwar Zamani

Kashi na Ɗaya

Sanar da Ɗalibanka

Yanzu da muka yi magana game da wasu dalilai na abun da zai sa ba za ka so kowa da kowa ya ga duk wani abun da kake yi a intanet ba, bari mu yi magana a kan yanda za mu kula da sirrinmu a intanet.

Kashi Na Biyu

Tattaunawa a Aji

A tsakanin tambayoyin, faɗaɗa tattaunawar ta hanyar yin amfani da bayanan da ke ƙasa a kan kowace tambaya.

Sanar da Ɗalibanka

Shin zai yiwu a samu saitunan sirri mabambanta na nau'o'in bayanai daban-daban?

1. Za ka iya yin la'aƙari da bayanai mabambanta a matsayin waɗanda suke da matakan sirri daban-daban. Za ka so ka raba hoton fuskarka, yin twitter game da siyasa ko addini, ko wani labarin mai ban dariya tare da masu sauraro mabambanta.

Yaya saitunan sirri daban-daban na mutane mabambanta? Misali, shin iyayenka / masu ba ka kulawa da kuma abokai na ganin abubuwa iri ɗaya a kan asusunka na dandalin sadarwar zamani?

1. Mahalarta taron ba za su so iyalinsu su iya yin jawabi a kan aikensu ba amma za su so abokansu su mayar da martani.

Shin za ka koma sannan ka sake duba duk wani abun da aka maƙala ka a ciki? Mene ne ko kuma me zai hana?

1. Za ka so ka cire duk wani abun da ke da kunyatarwa (misali., hoto daga wata ranar gashi mara kyau, wani hoto game da kai da ba ka so a raba).

A wani dandalin sadarwar zamanin, kamar Facebook, za ka iya canza saitunanka saboda ka tabbatar da wani abu kafin ya bayyana a kan furofayil ɗinka. Shin kana ganin wannan ra'ayin mai kyau ne? Mene ne, ko kuma me zai hana?

1. Zai ba ka damar taimakawa wajen kare abun da ke da kunyatarwa daga maƙala su a asusun dandalin sadarwar zamaninka. Duk da haka, ba zai tsayar da mutumin da ke aikewa da abun ba daga raba shi a kan asusunsu tare da abokansu / mabiya / mutanen da aka haɗa su da su.

Me yasa wani yake son ya taƙaita wanda zai iya duba su? Shin za ka iya bayar da misali?

1. Ba za ka so baƙi / mutanen da ba ka san su sosai ba su yi abota / bi / haɗuwa da kai a kan dandalin sadarwar zamani ko aiko maka da saƙonnin da ba a nema ba.

Shin kana abota da / mabiyan / an haɗa ka da iyayenka / masu bayar da kulawa a intanet? Malamai? Wasu manyan?

1. Shin wannan ya canza nau'in abun da kake rabawa ko kuma da wanda kake raba abubuwan?

Shin iyaye / masu bayar da kulawa ko malamai na buƙatar za ma abokai da / mabiyan / an haɗa su domin ka ga furofayil ɗinka?

1. Ya kamata mahalarta taron su yi la'aƙari da ko nasu saitunan sirrin za su ba kowa da kowa damar ganin furofayil ɗin dandalin sadarwar zamaninsu. Taimaka masu su yi tunani game da wasu hanyoyin da iyayi / masu bayar da kulawa ko malamai za su iya duba furofayil ɗinsu.

Yaya saitunan sirri daban-daban na dandalin sadarwar zamani mabambanta? A kan Twitter, shin twittarka a bayyane ta ke ga kowa da kowa ko a cikin sirri? Mutane nawa ne za su iya duba labaran Snap ɗinka? Mutane nawa ne za su iya samun damar shiga ɓangaren Instagram ɗinka? Shin wasu za su iya duba bidiyonka a YouTube? Shin mutane za su iya ganin hotunanka a Facebook, ba ya ga hoton furofayil ɗinka?

1. Idan mahalarta taron ba su sani ba, sanar da su cewa wannan yana da saitunan sirri.

Shin kana yin Twitter a ƙarƙashin sunanka na ainihi ko sunan da kake amfani da shi wajen wallafa abu? Me yasa?

1. Mahalarta taron ba za su so kowa da kowa ya san sunansu na ainihi ba. A cikin wannan yanayin, za su so su yi amfani da sunan da suke amfani da shi wajen wallafa abu.

Kashi Na Uku

Tattaunawa a Aji

Shirya maharta taron bibbiyu.

Sanar da Ɗalibanka

Mun san cewa saitunan sirri za su iya rikitarwa.

A cikin bibbiyunka, ɗauki wasu ‘yan mintuna domin ka samar da wata tambaya ko jawabi game da saitunan sirri.

Tattaunawa a Aji

Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su samar da wata tambaya ko jawabi game da saitunan sirri. Nemi su raba su raba tare da ƙungiyar gaba ɗaya sannan ka amsa duk tambayar da aka yi. Nemi wasu su samar da amsoshi daga mahalarta taron kafin ka bayar da amsarka.

Idan da akwai kwamfutoci ko na’urorin waya da ke da intanet, yi bayanin yanda za a kula da saitunan sirri a intanet.

Aiki

Jagora

Sanar da Ɗalibanka

Yanzu da muka yi magana a kan sirrin dandalin sadarwar zamani, bari mu faɗaɗa waccan ta hanyar bunƙasa wani jagora da za a iya yin amfani da shi wajen taimaka ma wasu domin su ƙara sani a kan abun da ka koya yanzu

A cikin mintuna 30 masu zuwa, ɗaya bayan ɗaya, ƙirƙiri wani jagorar da zai taimaka ma wasu:

1. Yi tunani game da masu sauraron aikensu a dandalin sadarwar zamani.

2. Zai nuna a kan abun da suke so su raba a bayyane da abun da suke so su sirrinta da kuma dalili.

3. Yi la’akari da dalilin da zai sa su sake dubawa da / ko a gyara saitunan sirrin dandalin sadarwar zamaninsu.

4. Gano yanda za su saita saitunan sirri daban-daban na abubuwa daban-daban da kuma dalilin da zai sa su yi hakan.

Wannan jagoran zai iya zama a cikin duk wani tsarin da kake so. Za ka iya rubuta jagora daga mataki zuwa mataki, ka tsara shi kamar “jagora ga mai yin amfani,” ka sanya hotuna ko zane, ko kuma duk wata hanyar da kake ganin za ta iya taimaka ma wasu su ƙara sanin waɗannan abubuwan; saki ranka don ka zama mai fasaha! A cikin wannan jagorar, ka tabbata ka:

1. Nunawa masu karatu yanda ake sake dubawa da kuma canza saitunan sirri a wannan dandalin sadarwar zamanin.

2. Samar da amsa ga wata tambaya game da saitunan sirrin da ka yi imanin cewa yana da muhimmanci, bisa la’akari da tattaunawar ƙungiyar da aka yi a baya.

Aiki

Ƙarfafawa mahalarta taron guiwa domin su zaɓi dandali daban-daban saboda a sakaya wasu dandalin a tare. Ba mahalarta taron mintuna 30 domin su kammala aikin.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarkashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarkashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein